




An yi wata giwa.

Giwa tana da raini.





Giwa ta raina kowa.

Ba ta jin kowa.



Giwa ta ga tulu.



Tulu na kan itace.

Giwa za ta sa hanci.

Zaki ya ce akwai



hatsari.

Giwa za ta sa hanci.

Kaza ta ce akwai


hatsari.

Giwa za ta sa hanci.


Kuda ya ce akwai

hatsari.



Giwa ta ƙi ji.

Giwa ta sa hanci.



Ashe ba tulu ba ne.

Gidan zuma ne.